Wanda aka haramtawa sauƙi to an haramta masa alheri

Daga Jabir - Allah Ya yarda da shi - daga Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Wanda aka haramtawa sauƙi to an haramta masa alheri".
[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana bada labarin cewa wanda aka haramtawa sauƙi to ba'a datar da shi ba a cikin al'amuran addini dana duniya haka da cikin abinda yake tasarrufi a cikinsa ga kansa, da kuma abinda yake tasarrufi a cikinsa tare da waninsa, to haƙiƙa an hana masa alheri gabaɗayansa.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/4939